BRAIN BUILDERS
YOUTH DEVELOPMENT
INITIATIVE

# Takardar Jagora ga 'yan Kasa domin Bibiyan Hakkokinsu




Sponsored by: LEAP AFRICA NIGERIA YOUTH FUTURES FUND

# Takardar Jagora ga 'yan Kasa domin Bibiyan Hakkokinsu

# Kunshiya


| | |
|---|---|
| Gabatarwa | 1 |
| Fahimtar Haƙƙoƙinmu da Nauye-Nauyenmu a Matsayin 'Yan Kasa | 3 |
| Ababen da 'Yan Kasa Za Su Ribata Bayan Zaɓe Domin Tabbatar da Gwamnati ta Sauke Nauyinta | 4 |
| Ruwa Da Tsakin 'Yan Kasa Da Yi Wa Gwamnati Matsin Lamba Kan Sauke Nauyinta ta Hanyar Dokar 'Yancin Bayani (FOI) | 5 |
| Ruwa Da Tsakin 'Yan Kasa da yi wa Gwamnati Matsin Lamba Domin Sauke Nauyinta ta Hanyar Saurarron Ra'ayin Al'umma | 9 |
| Ruwa Da Tsakin 'Yan Kasa Da Yi Wa Gwamnati Matsin Lamba Domin Sauke Nauyinta Ta Hanyar Taron Zauren Gari | 13 |
| Ruwa Da Tsakin Da 'Yan Kasa ke yi ta Hanyar Korafi Don Ganin Gwamnati ta Sauke Nauyinta | 16 |
| Ruwa Da Tsakin 'Yan Kasa ke yi Don Ganin Gwamnati ta Sauke Nauyinta ta Hanyar Hukunci | 21 |
| Ruwa Da Tsakin 'Yan Kasa ke yi Don Ganin Gwamnati ta bi Hanyar Amintaccen Tsarin 'Yan Kasa | 23 |
| Kammalawa | 26 |
| Karin Bayanai | 27 |

# Gabatarwa

Bayan zaɓukan da suka gabata a Najeriya na ranar 25 ga Fabrairu, 2023, da kuma ranar 18 ga Maris, 2023, Zaɓaɓɓen Shugaban Ƙasa, Zaɓaɓɓen Mataimakin Shugaban Kasa, da sauran zaɓaɓɓun shugabanni sun fara aiki. An rantsar da Shugaban Kasa da mataimakinsa ne a ranar 29 ga Mayu, 2023, yayin da aka rantsar da 'yan Majalisar Dokokin Tarayya a ranar 11 ga watan Yuni, 2023.

Ana sa ran Zaɓaɓɓen Shugaban Kasa, Mataimakin Shugaban Kasa, gwamnoni, da mataimakansu za su yi mulki ne tsawon shekaru huɗu, wanda zai soma tun daga ranar da aka rantsar da su. Sai dai duk da haka, ana iya maye gurbinsu idan aka tsige su, ko sukayi murabus, ko kuma idan sun mutu. Mataimakin Shugaban Kasa ko Mataimakin Gwamna ne zai maye wannan gurbi idan irin wannan lamari ya kasance.

Dangane da Zaɓaɓɓun 'yan majalisar, su ma ana sa ran za su yi mulki na wa'adin shekaru huɗu bayan rantsar da su a zaman farko na majalisar. Idan an zaɓi dan majalisa ta hanyar zaɓe na musamman (wanda aka sani da zaɓen cike-gurbi), wa'adinsu zai kare da zaman majalisa na yanzu. Akwai yanayi da dan majalisa ba zai iya kammala wa'adinsa ba, kamar misali idan ya mutu, ko kuma idan mafi rinjayen masu kaɗa Kuri'a a mazaɓarsa sun yi masa kiranye, ko kuma idan kotu ta same shi da wani mugun laifi.

A duk lokacin da aka samu wani gurbi, Hukumar Zaɓe ta Kasa (INEC) ce ke da alhakin gudanar da zaɓen maye gurbi cikin kwanaki 90 domin cike wannan gurbi.

**Zaɓe na taka muhimmiyar rawa a tsarin dimokuraɗiyya, koda yake hakan ba ya nuna tabbacin tasirin 'yan ƙasa, wajen tsara manufofi ko gudanar da mulkin ba. Duk da haka, tsarin yana ba wa 'yan ƙasa damar zaɓen jagororinsu sannan su yi ruwa da tsaki wajen yanke shawarwari. Akwai buƙatar a rika kallon zaɓe a matsayin wata dama ta ƙarfafa wa 'yan Ƙasa da ankarar da su a kan muhimmancin shiga a dama da su da kuma zaburar da zaɓaɓɓun jami'ai kan hakkin da ya rataya a wuyansu.**

Haka kuma, yana da muhimmanci a tabbatar da cewa 'yan ƙasa sun dage wajen yin ruwa da tsaki ta fannin bibiyan masu rike da madafun iko har sai sun sauke nauyin da ya rataya a wuyansu. Za su yi hakan ne ta hanyar shiga a dama da su a harkokin siyasa ta yadda za su taimaka wajen tsara manufofin gwamnati da kuma tabbatar da an yi amfani da dukiyar ƙasa ta hanyar da ta dace.



# Fahimtar Yanci Da Kuma Haƙƙin Dake Kanmu A Matsayin Mu Na 'Yan Ƙasa


'Yan ƙasa na da haƙƙoƙi da nauye-nauye, waɗanda suka haɗa da 'yancin shiga a yanke shawarwarin da suka shafi al'ummominsu. 'Yan ƙasa na da yanci da kuma hakki, waɗanda suka haɗa da 'yancin shiga da yanke shawara da suka shafi al'umman su. Muhimmancin tsayuwa a kan haka bai takaita ga dimokuraɗiyya ba, har ma yana tasiri wajen haifar da sauye-sauye masu nagarta a cikin al'umma da kuma bai wa 'yan ƙasa ƙwarin gwiwa. Gudumawa da saka bakin 'yan ƙasa yana da mahimmanci a lokacin zabe da tsakanin zaɓuka, kuma ana iya aiwatar da hakan ta hanyoyi daban-daban kamar cibiyoyin sadarwa mallakar ƙasa, ƙungiyoyi masu zaman kansu, da kuma dandalin shafukan sada zumunta.

Domin tabbatar da sauke duk wani nauyi, dole ne 'yan ƙasa su shiga a dama da su a harkokin siyasa. Za su iya neman jagoranci nagari sannan su tabbatar masu riƙe da madafun ikon sun cika alƙawura tare da sauke hakki da nauyin da rataya a wuyansu. Domin tabbatar da cewa an ɗora tsarin dimokuraɗiyya akan turba madaidaiciya, ya kamata dukkan 'yan ƙasa da masu ruwa da tsaki a harkokin siyasa su shiga a dama da su a duk ɓangarorin da suka danganci yanke shawarwari na siyasa, ciki har da tsare-tsaren zaɓen, wanzar da zaman lafiya da kuma kafuwar tsarin mulki.

A yau, 'yan ƙasa sun shige gaba wajen kawo sauye sauye ta hanyar amfani da sabbin dabaru na yin ruwa da tsaki da kuma wakilci. Suna neman samun tasirin gaske a kan wakilan ƙungiyoyi da faɗaɗa hanyoyin sauke hakkokin da suka rataya a wuyan gwamnati da kuma ƙara kaimi a fagen yin ruwa da tsaki, bayan jefa ƙuri'a kawai a lokacin zaɓe.Da taimakon fasahar zamani yan kasa zasu bayyana ra'ayoyinsu a bayya fannin musayar yawu a cikin jama'a da ke da daman tsara manufofi da makomar siyasa. Wannan haɓaka ta gudumawar 'yan ƙasa da sha'awar kara kusanci tsakanin 'yan ƙasar da 'yan siyasa, yana ƙara buɗe ƙafofin kawo tsare-tsare da sauye-sauye musamman tun daga tushe.

Ya kamata 'yan ƙasa su fahimci muhimmancin tasirin da suke da shi sannan su taka rawa wajen inganta al'ummansu da kuma manufofin da za su shafi rayuwarsu. 'Yan ƙasa na iya kawo sauyi mai ma'ana tare da tabbatar da isar da muryoyinsu ta hanyar yin ruwa da tsaki a harkokin siyasa.





# Abubuwan Da ‘Yan Kasa Za Su Ribantu Da Shi Bayan Za Be Domin Tabbatar Da Gwamnati Ta Sauke Nauyinta

**Dokar 'Yancin (Neman) Bayani**

**Yarjejeniyar ‘Yan ƙasa**

**Sauraron Ra'ayin Jama'a**

**Hukumomin Shari'a**

**Korafe-Korafen Yanar Gizo**

**Tarukan Zauren Al'umma**



# Ruwa Da Tsakin 'Yan ƙasa Da Matsawa Gwamnati Lamba Kan Sauke Nauyinta Ta Hanyar Dokar 'Yancin Bayani (FOI):

A ranar 28 ga watan Mayun shekarar 2011 ne tsohon Shugaban Kasa Goodluck Ebele Jonathan ya rattaba hannu kan Dokar 'Yancin Bayani ta Najeriya a matsayin dokar da ta ba wa jama'a damar samun bayanai a kan al'amuran da ya shafesu daga hukumomin gwamnati.

A sashe na 32 na kundin takardun dokar, ta kuma nemi kare bayanan jama'a da bayanan da suka shafesu don kare jama'a da kuma kare jami'an gwamnati daga azabtarwa ko gurfanar da su kan bayyana wasu nau'ukan bayanan hukuma ba tare da izini ba.

A cikin gabatarwar ta, Dokar ta bayyana a takaice - Dokar da za ta samar da bayanan da jama'a ke nema cikin sauki, bai wa jama'a damar amfani da bayanan, kare bayanan jama'a gwargwadon bukatun jama'a da kuma kare sirrikansu, kare jami'an gwamnati daga fuskantar tsattsauran mataki na bayyana wasu nau'ikan bayanan hukuma ba tare da izini ba da kuma kafa hanyoyin cimma nasarar waɗancan dalilai da sauran al'amura masu alaƙa dasu.

Daga bayana nen da ke sama, a bayyane yake cewa dokar ta FOI ta rushe wasu dokoki kamar Dokar Sirrin Gwamnati da kuma Kundin Laifuffuka da suka kafa dokar hana bayyana bayanan jama'a ba tare da izini ba. Hasali ma, a matsayin Dokar Tarayyar Najeriya, tanade-tanaden Dokar 'Yancin Bayanai ya wuce na duk wata doka da ake da ita dangane da ɓoyewa da bayyana bayanan jama'a a Najeriya.

# Hanyoyin Yadda Ake Amfani Da Dokar ʻYancin Bayani (FOI)[1]

## Aiwatar da bincike

Da farko, buƙatun Dokar ʼYancin Bayanin da suka fi nasara sun fi mayar da hankali ne akan bincike nagartacce kuma na haƙiƙa.Anfi son ayi amfani da shine kawai don neman bayanen da basu samuwa a fili. Kafin a rubuta wasiƙar FOIA, ya kamata a yi bincike don sanin irin bayanan da ake nema, waɗanne hukumomi ne ke da hurumin bayar da bayanen, kuma waɗanne bayanan gwamnati za ta dauka kan bayanan da ake shaʼawar samu wadanda dama akwai su a wurin jamaʼa. Da zarar an gano bayanin da ake neman ba ya samuwa a bainar jama'a, ya kamata a bincika takamaiman bayanen da aƙe buƙatan, nauʼukan bayanen, ko wasu batutuwan da kuke son nema. Duk sassan reshen zartarwa da hukumomi suna ƙarƙashin Dokar FOIA. Sai dai Dokar ta FOI ba aiki a kan Majalisar Dokoki ta Kasa da kotuna, maʼana ba zaʼa iya aika wasiƙar FOI zuwa kotu ko Majalisar Dokoki ta Kasa ba. A aika rubutacciyar wasiƙarku zuwa ga shugaban hukumar sashen da lamarin ya shafa..

## Rubuta Wasiƙar neman FOI

Buƙatar Dokar FOI tana ɗaukar sigar kyakkyawan tsari a wannan matakin. Bayan gudanar da bincike kan irin bayanin da za ku nema daga hukumomi, to daga nan an shirya don rubuta wasiƙar buƙatar Dokar FOI. Ku aika wasiƙar ku, a tabbatar an zaɓi haƙiƙanin hukumar ta hanyar gano wadanne hukumomin gwamnati ne ke ƙarƙashin FOIA, sannan sai a tsara haƙiƙanin bayanan da ake buƙata. Dukkan hukumomi suna karɓar wasiƙun ta saƙon gidan waya. Hukumomi da yawa kuma suna karbar buƙatun da aka aika ta hanyar aika saƙon Fax ko Imel. Wasu hukumomi suna da fom ɗin shigar da buƙatar ta yanar gizo.

## Miƙa Wasiƙar Buƙatar ku ta FOI

A miƙa buƙatar ga hukumomin gwamnati waɗanda ke ƙarƙashin Dokar FOI (FOI ta shafi duka cibiyoyin jihohi da na tarayya), da kuma tsara takamaiman buƙatun da aka yi niyya. Duk hukumomi suna karɓar buƙatun ta saƙon gidan waya. Hukumomi da yawa kuma suna karɓar buƙatun da aka aika ta fax ko imel. Wasu hukumomi suna da fom ɗin miƙa buƙatar ta yanar gizo.

[1] https://ymonitor.org/request-guide/

## Bibiyar Wasiƙar Buƙatar ku ta FOI

Da zarar kun cika rubuta wasiƙar buƙatun ku, yana da muhimmanci ariƙe bayanan da suka dace kamar kwanan watan da aka aika, hukuma da aka aikawa ko wasu ababe, batun (batutuwa), lambobin bin diddigin hukumar, kwanan wata da yanayin kowane wakilin hukumar, gami da lambar waya da adireshin imel. Wannan bayanin yana da muhimmanci wajen bin diddigin tambayoyin, ƙarin bayani, da ƙararraki da neman taimako don guje wa maimaici wajen aika buƙatun

Bayan kun miƙa buƙatar ku ta FOI, daga nan za a soma zaman jira. A bisa tanadin doka, hukumomi za su fitar da ƙudiri na ƙarshe a cikin kwanaki bakwai (7) na ranakun aiki, amma yawancin bangarorin FOI na hukumomi suna da tarin kwantan buƙatu a wurinsu.

## Amsar Wasiƙar Buƙatar ku ta FOI

Za ku sami amsa - wasiƙar amincewa ko kawo bayanan buƙatun abin da zai iya jinkirta aiwatar da buƙatunku, ko kuma za a iya aiwatar da bukatun gaba ɗaya ko a kashi-kashi (an gyara). Haka kuma, za su iya ƙin tabbatarwa ko ƙaryata cewa suna da bayanan, ko ƙin yarda da buƙatun saboda wasu dalilai da ke ƙarƙashin tsare-tsarensu - Idan sunyi fatali da bukatarku, za ku iya yanke shawarar roko ta hanyar rubuta wata wasiƙar shigar da buƙatar sannan a aika wa hukumar. Idan ba ku gamsu da hukuncin da kuka ɗauka ba, kuna da damar shigar da ƙara a wata kotun tarayya domin a saki ƙunshin bayanan.

## Amfani da Dokar FOI yadda ya kamata

Domin amfani da wannan bayanin da aka aiko muku, da fatan za a yi abin da ya kamata. A nemi izini idan za ku sake wallafa wasu ƙunshin bayanan da aka aiko muku (ko aƙalla a yarda da salsalarsa). Duk da cewa an aiko muku da bayanin, haƙƙin mallaka na yau da kullun zai kasance na hukumar da abin ya shafa ko kuma wanda ya ba su.

## Misalin Wasikar Neman 'Yancin Bayani[2]

Sunanka
Adirishinka
Lambar-wayarka
Adireshin akwatin imel
Kwanan wata

Zuwa ga Jami'in 'Yancin Bayanai

*((Haka nan kuna iya zaɓar aika wasiƙar zuwa ga shugaban cibiya, wato: Babban Sakatare, idan wata ma'aikata ce; ko zuwa ga Darakta-Janar, idan wata hukuma ce; ko kuma Baban Manaja, idan wani kamfani)*

Sunan-Ma'aikata

Adireshin Ma'aikata

Ya mai girma Jami'in 'Yancin Bayanai,

**Neman Bayani / Ajiyayyen Bayani / Takardu a ƙarƙashin Dokar 'Yancin Karban Bayanai**

Bisa tanadin Dokar 'Yancin Bayani ta 2011, Ina neman kwafin waɗannan takardu masu zuwa:

1. Kwafin bayanan taron kwamitin tsare-tsare na Ma'aikatar Harkokin Cikin Gida wanda aka gudanar a ranar 28 ga Mayu, 2011, inda aka yanke shawarar sayen kwamfutoci na tafi-da-gidanka guda 250 ga manyan jami'an ma'aikatar.
2. Kwafin dukkan wasiƙun da suka hada da imel, tsakanin jami'an Ma'aikatar Yada Labarai da kamfanin da aka fi sani da Blue Skies International, daga ranar 1 ga watan Junairun shekarar 2011 zuwa 30 ga watan Yuni, 2011, wanda ya kai ga rattaba hannu kan yarjejeniyar fahimtar juna a ranar 1 ga Yuli. 2011.
3. Jerin duk tsare-tsaren gini da aka amincewa da kuma izinin da Ma'aikatar Tsare-Tsaren Birane ta bayar tsakanin 29 ga Mayu, 2007 da Mayu 28, 2011. Ana buƙatar jerin bayanan ya nuna sunan mai nema, kwanan watan ranar gabatar da bukata da kwanan wata ranar da aka amince, nau'in ginin da aka amince da kuma adadin kuɗin da aka caji kowane mai nema.

Zan kasance mai godiya idan za ku iya ba ni kwafin waɗannan takardu

Idan kuna buƙatar wani karin bayani game da wannan buƙatu, ina fatan ba za ku yi jinkirin tuntuɓa ta ta waya (lambar wayar ku) ko ta imel (adireshin imel ɗin ku).

Ina fatan samun waɗannan takaddun cikin gaggawa kuma, a kowane hali, cikin kwanaki 7 na karɓar wannan bukatu, kamar yadda Dokar 'Yancin Bayani ta 2011 ta tanadar.

Naku har kullum,

Sa hannu

Sunan ku

[2]

# Ruwa Da Tsakin 'Yan Kasa Da Matsawa Gwamnati Lamba Domin Sauke Nauyinta Ta Hanyar Sauraron Ra'ayin Al'umma

Taron sauraron ra'ayin al'umma wani budadden taro ne na 'yan majalisa, 'yan ƙasa, masu ruwa da tsaki, da jami'an gwamnati domin tattaunawa, muhawara da ba da shawarwari ga wata doka da ake so a Majalisa. Yana ba da dama domin samun ra'ayin jama'a game da wasu muhimman manufofi na majalisa ko dokoki da suka shafi 'yan ƙasa da dama, kamar nazarin tsarin mulki ko kasafin kuɗi na shekara. Yana bai wa wani rukuni na 'yan ƙasa damar sadar da buƙatunsu ga 'yan majalisa. Sauraron ra'ayin jama'a yana buƙatar tattaunawa ta gaskiya da mutunta juna tsakanin 'yan majalisa, jami'an gwamnati, masu ruwa da tsaki da 'yan ƙasa baki daya.

'Yan kasa na iya shiga tare da kawo gagarumin sauyi yayin sauraron ra'ayin jama'a da kuma bayan taron. Na farko, a yayin taron sauraron ra'ayin jama'a, za a iya gabatar da wata takarda mai dauke da batutuwan da ke buƙatar kulawa cikin gaggawa da kuma sassan da ke buƙatar a yi watsi da su. Kwamitin zai ba da izinin gabatar da bukatar da tofa albarkacin baki ga waɗanda suka nuna sha'awarsu. Masu sha'awar – ɗaiɗaikun mutane, wata ƙungiya ko ƙungiyoyi za su iya aika yarjejeniyar ta kan layin na'ura.

## Waɗanne hanyoyi ne 'yan ƙasa za su bi domin shiga taron sauraron ra'ayin jama'a?

01 Lalubo/Binciƙo bayanai a jaridu, gidan talabijin, tallace-tallace a gidajen rediyo, ko dandalin sada zumunta ta yanar gizo don sanin lokacin da kuma inda aka shirya taron sauraron jama'ar gari.

02 A sanar da ku kan Dokar da za a tattauna kuma a sami kwafin Kudirin wannan doka (A Majalisar Dokoki ta Kasa ko Majalisar Jiha)

03 Gano batutuwa masu fifiko kuma ku tsara shawarwarinku daidai da batutuwan. Haka nan, za ku iya haɗawa da batun da kuke da yakinin ya kamata a magance shi wanda ba a haɗa shi ba a ƙunshin ƙudirin.

04 Tsara bayanan da ke ba da cikakkun ra'ayoyinku da shawarwarinku. Gabatar da kwafin bayanan kafin a soma sauraron ra'ayin jama'a.

05 Halartar majalisin sauraron ra'ayin jama'a kuma ku gabatar da duk ra'ayin ku.

## SHIN SAKAMAKON SA HANNU DA YIN RUWA DA TSAKI ZAI IYA YIN TASIRI?

Eh, ta hanyar bayar da shawarwari, yin kamun-kafa, sanya hannu kan takardar koke, zanga-zangar lumana, da kuma ci gaba da gabatar da buƙata ga 'yan majalisa.

### Tsarin Amincewa Da Yarjejeniya

Wannan tsarin amincewa da yarjejeniya shi zai taimaka maka ko ma'aikata tsara yadda za a ƙulla yarjejeniya.

Suna/Sunan Ma'aikata/Kamfani

Adireshi

Lambar Waya/Adireshin akwatin imel

**Gabatarwa**

Ana bukatar wannan ya ƙunshi bayani game da ku / ƙungiyar ku / kamfanin ku, dalilin da yasa ku / ƙungiyar ku / kamfanin ku ke sha'awar dokar, bayyana muhimman batutuwa da shawarwari. Haka kuma ya kamata ku bayyana dalilin da ya sa gyaran da aka tsara ke da muhimmanci. Idan kuna tunanin gyaran ba shi da muhimmanci, kuna iya bayyana shi kuma ku bayyana dalilin da ya sa kuka gaskata rashin muhimmancinsa.
Shawara: Bayyana manufa kai tsaye kuma a sauƙaƙe.

Hujja da shawarwari

An buƙaci wannan ɓangaren ya ƙunshi gyare-gyare da shawarwinku/ ƙungiyar ku / ma'aikatar dangane da kudirin ko batun. Ya kamata a nan a ba da shawarwari da za a yi la'akari wajen gyara ko watsi da wani sashe ko gabatar da sabon sashe a cikin Kundin Tsarin Mulki ko kudirin da aka gabatar.
**Shawara:** A tabbatar an faɗi ko an ambaci sassan da suka dace da za su ƙarfafa wa hujjarku.

**Kammalawa**

A wannan sashe kuma za a bayyana wa kwamiti dalilan ku ko ƙungiyar ku ko ma'aikatarku kan daukar shawarwarinku.

# Dabarun Yadda Za A Gabatar Da Buƙatu A Zaman Sauraron Ra'ayin AL’UMMAR GARI



## Gaisuwa

Za a fara da shimfiɗa gaisuwa ga 'yan majalisa da sauran masu ruwa da tsaki (wannan na iya haɗawa da wakilan hukumomin gwamnati, masu ruwa da tsaki, kafafen yada labarai da sauran jama'a) da suka halarci taron. Sai dai kuma, idan ba za ku iya kiyaye wannan ƙa'idar ta wannan shimfiɗa ta gaisuwa da kyau ba, to zai fi kyau kawai ku yi gaisuwa ta gama-gari tare da cewa: “Ba ni damar tsayawa kan ƙa'idar gabatar da gaisuwa da aka riga aka shimfiɗa” ko “ba zan iya kiyaye ƙa'idar da aka riga aka tanada ba.”



## Gabatar da kanka da ƙungiya ko ma'aikata

Faɗi sunanka, ma'aikatar ka, da sunan muƙaminka. Idan kana magana ne a ƙashin-kanka, sunanka kaɗai ya wadatar.



## Bayyana batun a taƙaice

tare da hikaito sashe ko sassa, ko wuraren da ke cikin batutuwanku. Galibi a ajandar sauraron ra'ayoyin yana ƙunshe ne da jerin sunaye ko ƙungiyoyin da za su gabatar da jawabi. Saboda haka ana so ka taƙaice jawabinka kuma a yi a sauƙaƙe. A wasu lokutan domin bai wa jama'a da yawa dama su bayyana nasu ra'ayin, a kan ɗebar wa kowane mai jawabi tsawon lokacin da bai wuce minti uku zuwa biyar ba. A KIYAYE WANNAN TANADIN. A TSAYA KAN MUHIMMAN HUJJOJI DA SHAWARWARI.



## Rufewa

Yin godiya ga 'yan majalisa da sauran mahalarta taron dangane da sauraron da suka yi. Ana iya rufewa da faɗakarwa; Misali shi ne: “Ina fata wannan Kwamitin zai yi la'akari da duk abubuwan da aka gabatar da su a cikin bayanin namu kuma muna fatan zai samar wa 'yan Najeriya ko Jihar ku wani ƙudiri da duk za mu yi alfahari da shi.”

# Jajircewa, Yin Ruwa Da Tsakin , Saka Idon 'Yan Kasa Da Yi Wa Gwamnati Matsin Lamba Domin Sauke Nauyinta Ta Hanyar Taron Sauraron Jama'an Gari

Taron zauren gari wani taro ne na jama'a na yau da kullun da ake gudanarwa game da batutuwan da suka shafi kowa. Tun tsawon shekaru da dama, tarurrukan zauren gari sun kasance muhimmin al'amari na sanar da 'yan ƙasa game da batutuwan da suka kunno kai, auna matsayar al'umma kan wasu batutuwa da kuma zama wani majalisi na nazari da aiwatar da hanyoyin magance matsaloli. Waɗannan tarurrukan kuma suna zama wata babbar hanya domin isar da saƙonni ga jama'a, samar da bayanai ga kafofin watsa labarai, assasa wani yunƙuri na bayar da shawarwari da wayar da kai ta hanyar tattarawa da shirya tallafin al'umma da gano daidaikun mutane da ƙungiyoyi saboda samun haɗin gwiwa a gaba.

## SHIRYA TARON SAURARON JAMA'AN GARI

MATAKI NA 01

### Assasa Kwamitin Tsare-Tsare

Mafi kyawun hanyar da za ta sa taronku ya yi nasara gwargwadon hali shi ne assasa haɗin gwiwa tare da ƙungiyoyi daban-daban da abokan hulɗa a cikin al'umma, kuma ku yi aiki tare da su wajen tsarawa da gudanar da taron ku. Waɗannan alaƙoƙi za su daukaka martabar taron zauren garin ku da kuma kara wayar da kan jama'a da janyo hankalinsu.

MATAKI NA 02

### Binciko Ɗabi'u na Musamman na Al'ummarku

Kafin shirya taron zauren garinku, yana da muhimmanci ku fahimci waɗansu al'amura na musamman na al'ummarku, ƙalubale da damarmarkin da suke da su. Sai a yi bitar bayanai iri-iri da tattara bayanan al'umma bayan gudanar da ingantaccen bincike. Wannan bayanin zai taimaka muku sanin yadda za ku mayar da hankali kan abubuwan da za ku tattauna da kuma tabbatar da amincewarsu yayin gabatarwa.

MATAKI NA 03

### Gano Manufofinku

Babu taron zauren gari guda biyu da suke kamanceceniya da juna. Abubuwan da ke cikin taron ku, tsari da manufofinku za su dogara takamaimai kan buƙatun da ku da abokan hulɗar ku kuka gano. Misali, manufofinku na iya zama kawai sanar da mambobin al'umma game da wata matsala a cikin al'umma. Wasu al'ummomi na iya gudanar da taron zauren garinsu ya zama dandalin kira zuwa ga wasu aiyuka, kamar inganta ayyukan kiwon lafiya, ilimi ko abubuwan more rayuwa.

# Gudanar Da Taron Zauren Gari

MATAKI NA 01

## Tsara Taron ku

Domin tabbatar da nasarar taron, a sanya mambobin al'umma da masu ba da gudunmuwa a matakan ayyuka daban-daban.

**Tsarawa:** Ya kamata wasu mutane su yi sammako domin tabbatar da wurin (misali wani dandali ko ɗakin taro ko kuma wani zaure ko ma a ƙarƙashin bishiya) an tsara shi yadda ya kamata sannan idan akwai buƙatar aiwatar da wani sauyi na ƙarshe. Dangane da manyan tarurruka, ƙila kuna buƙatar samun na'urorin sauti, ciki har da makirufon da za su rika amsa-kuwar masu jawabi. Amma idan ƙananan tarurruka ne, wanda mahalartan ba za su wuce 25 ko ƙasa da haka ba, za a iya shirya taron a gudanar a zaune a kan tebur.

**Wurin samun izinin shiga/daukar sunayen mahalarta/rajista:** Ana buƙatar a tanadi wani teburin a wurin shiga taron, inda za ku iya tattara sunaye da bayanan tuntuɓar duk wanda ya zo ya karbi wasu kayan. A tuna cewa za a yi tanadin takardun daukar sunayen mahalarta daban daban, ɗaya saboda gama-gari, ɗaya kuma na wakilan kafofin watsa labarai. Wannan bayanin zai zamo mai muhimmanci a yayin da kuke gudanar da ayyukan ku na bin diddigi da kuma tsara tarurruka na gaba.

**Kunshin bayanai:** A teburin neman izinin shiga, kuna iya tanadar da ajandar wannan taro da sauran bayanai, da kuma kayan aiki na daukar rahoto domin ma'aikatan jarida. Idan kuna da wani shiri na tattaunawa kan wasu takamaiman batutuwa, to a tanadi kwafi-kwafi na takardun da ke ƙunshe da bayanai ko batutuwan.

MATAKI NA 02

## Gudanar da Taron ku

Ya kamata a fara taron da maraba da gabatarwa daga kwamitin tsare-tsare na masu shirya taron zauren gari. Bai kamata a shafe tsawon lokacifiye da minti biyar ba wajen yi wa mahalarta maraba da gabatarwa sannan kuma a bayyana maƙasudin gudanar da taron da yi wa baƙi maraba da kuma gabatar da mai gudanarwa da tsawatarwa a taron. Daga nan sai mai gudanarwar ya buɗe taron zauren garin da dan takaitaccen bayani kan batutuwan da za a tattauna, da bitar tsarin da za a bi da kuma gabatar da dukkan wadanda za su yi jawabi. A mafi akasarin lokuta, ya fi kyau a fara bai wa kowane mai jawabi ya gabatar da jawabinsa sannan a bai wa kowannesu mintuna uku-uku domin amsa tambayoyi daga mai gudanarwa. Kada a bari a shafe fiye da mintuna hamsin ana wannan tattaunawa. Bayan masu jawabi sun kammala, daga nan sai mai gabatarwa ya shiga fagen tambayoyi da amsoshi. Bayan an kammala tambayoyi da amsoshi, ko dai mai gabatarwa ko kuma wani daga cikin waɗanda suka shirya taron, su gabatar da jawabin rufe taron tare da yin godiya ga dukkan wadanda suka samu damar halartar taron. Yana mai ƙarfafa gwiwar mahalarta taron da su yi yunƙuri wajen daukar mataki na farko – mataki daya komai kankantarsa. Karfafa wa wadanda suke son jagoranci, samun jagorori da kuma kafa wata 'yar karamar kungiya domin daukar karin wasu matakai. Sannan kuma a bayar da bayanan tuntuɓa domin waɗanda ke son ƙarin haske ko bin diddigi a kan wasu batutuwa bayan an kammala taron.

MATAKI NA 03

## Buɗe ƙofar Tattaunawa da manema labarai

Yana da kyau a samu isasshen lokaci bayan an kammala taron domin amsa tambayoyin manema labarai. Alal akalli, yana da kyau a keɓe minti 30 a ƙarshen lokacin tambayoyi da amsoshin don amsa tambayoyin 'yan jarida da masu magana da yawun ku. A lokuta da yawa, kafofin watsa labaru za su buƙaci yin hira daga baya, don haka a tabbatar da cewa a kodayaushe akwai wanda zai kula da buƙatun tambayoyin kafofin watsa labarai.

# Bayan Taro: Mene Ne Abu Na Gaba Da Za A Yi

Gwagwarmayar bata ƙare tare da taron zauren gari ba. A mafi yawan lokuta taron yana zama mai ingiza dabaru da tsare-tsare na gaba. Domin ganin an cimma buri, kuna buƙatar gudanar da matakai masu yawa a cikin makonni da za su biyo bayan taron.

MATAKI NA 01

## Gudanar da Tattaunawa

Bayan ƙasa da makonni biyu da gudanar da taron majalisar garin, sai ku sake tara manyan mutanen da ke da hannu wajen tsara taron inda za a yi bita tare da tattauna yadda taron ya gudana. A bincika ko kun cimma manufofin ku da kuma yadda kuke son aiwatar da bayanai da ra'ayoyin da suka fito a aikace a cikin al'umma.

MATAKI NA 02

## Samar da Tsarin Aiki

Bayan kammala taron, sai a rubuta sharhin da aka yi daga taron zauren gari, tare da ba da cikakken bayani game da taron da kuma bayyana matsaloli da mafita da al'umma da masu jawabi suka gabatar a takaice. A yi nazari game da abin da matakai na gaba za su iya zama sannan a tsara hanyoyin aiki. Wasu ra'ayoyin shawarwari a kan manufofi, yaɗa bayanai ko wayar da kan jama'a.

MATAKI NA 03

## Amfani da Taron Zauren Gari Wajen Gina Tsarin Isar da Koken Jama'a Ga Hukumomi:

Ɗaya daga cikin mafi amfanin shawarwarin da za ku iya samarwa daga taron ku shi ne jerin sunaye da bayanan tuntuɓar dukkan wanda ya halarta. Wannan bayanan na iya taimaka muku aika wasiku don taruka da shirye-shirye da zaku iya a gaba da kuma kasancewa hanyar samun magoya baya da 'yan sa kai a lamarin. Har ila yau, kundin bayanai da aka ajiye a na'ura na iya zama wata hanya don gano mutanen da za su yi sha'awar sanya hannu kan koke don halartar taron jama'a.

# Ruwa Da Tsakin Da 'yan Kasa Ke Yi Ta Hanyar Ƙorafi Don Ganin Gwamnati Ta Sauke Nauyinta

Korafe-korafe hanya ce mai kyau don haifar da canji mai ma'ana a duniya. Ko da batu ne mai sarƙaƙiya a duniya ko kuma zaɓe na cikin gida mai sauƙi, korafi na iya isar da sakonku kuma ya samar da sakamako na gaske. Duk da yake ƙirƙirar ƙorafi na iya zama sau da yawa kamar aiki mai ban tsoro da ban mamaki, a zahiri yana da sauƙin farawa. Abin da kawai za ku yi shi ne a zaɓi dandalin sadarwa da ya dace, a rubuta takardar ƙorafi, kuma masu bibiyarku su saka hannu a kaii.

Gano manufarku da masu sauraron da kuke so. Kowanne ƙorafi nada manufa daban, masu sauraro daban, da kuma irin canjin da kuke son gani. Sanin abin da kuke so ku canza da wadanda kuke buƙatar isa garesu zai taimaka sosai yayin da kuke tsara korafinku.

**Dandalin sadarwa ita ce hanyar da kuke amfani da ita don ƙirƙira da rarraba ƙorafin ku. Don zaɓar dandalin, ya kamata ku yi tunanin wanda kuke buƙatar isarwa da sakon abin da kuke son canzawa.**

**Wasu hukumomi da cibiyoyi na gwamnati suna buƙatar takamaiman adadin sa hannu kafin su yi la'akari da korafin da za a yi. Ku tabbatar da cewa kun bincika don ganin irin dandalin da suke ba da izini da sa hannun, sannan sa hannu nawa za ku buƙata a zahiri kafin farawa.**

## Zaɓi tsakanin ƙorafin da aka wallafa ta intanet da wanda aka yi a takarda bisa takamaiman buƙatunku

**Zaɓin dandalin da ya dace zai tabbatar da cewa masu sauraron da suka dace suna gani kuma suna sanya hannu kan takardar ƙorafi. Yi amfani da dandamalin sadarwa na intanet idan kuna buƙatar isar da sakon ga mutane daga sassa daban-daban na duniya. Yi amfani da samfuri don wallafa kwafi na zahirin takardar idan kuna ƙoƙarin yin kira ga al'ummar yankinku.**

**Zai fi sauƙi a sa mutane su sa hannu a takardar ƙorafinku idan za ku iya gabatar da ita kai tsaye ba tare da tura sako ba, kuma ku bayyana musu dalilinku. Yi la'akari da buga takardar korafi da gabatar da ita ga jama'a da kanku.**

## Yi amfani da dandalin sadarwar intanet don ƙirƙirar ƙorafi ta yanar gizo.

**Akwai shahararrun shafukan sadarwa da yawa waɗanda zaku iya amfani da su don gabatar da korafinku. Change.org, GoPetition.com, da iPetitions dandalin sadarwar intanet ne masu sauƙi na yanar gizo waɗanda ke ba ku damar wallafa korafi da raba su ta hanyar na'urar intanet. Suna da 'yanci a yi amfani da su, amma suna da iyaka wajen zaɓan irin ƙorafin da aka tsara a yi.**

A cewar change.org[4]. 'Korafi rubutaccen takarda ne da ake neman wani nau'in canji ko buƙatar da aka yi wa wani adadi. Samun sa hannu da yawa daga mutane daban-daban yana nuna ƙimar goyan baya ga korafinku'.

**Asalin tsari wajen yin ƙorafi ya haɗa da:**




[4] https://guide.change.org/create-a-petition

## Zaɓi batun ka

Mataki na farko na rubuta ƙorafi shi ne zaɓar batun da ake son yi, zaɓar batu na nufin batu da ke da ma'ana a gare ku. Idan baku da takamaiman batun da kuke son gabatarwa a zuciya, ku fara da yin tunani game da abubuwan da kuke sha'awa masu fadi, kamar walwalar dabbobi. Sa'an nan, ku yi tunani game da yadda za a rage batun ku zuwa wani takamaiman abu da ake son aiki a kai. Ku Kirƙiri tsari ba kawai kan abinda kuke so ya faru ba, har ma da yadda za ku cimma manufarku da kuma yadda za ku auna nasararsa. Gwargwadon cikakken bayani, gwargwadon kyawunsa. - kuna son ɗaukar hankalin masu karatu kuma ku shawo kansu don sanya hannu kan takardar ƙorafin. Ta hanyar zaɓar batu mai jan hankali tare da bayyanannun matakai, za ku saita alkiblar nasarar kamfe din korafinku wanda zai janyo sa hannu masu yawa.

## Rubuta taken batun

Taken batun shi ne damarku ta farko don jawo hankalin masu karatu kan ƙorafinku tare da bayyana irin canjin da kuke son cimmawa.

Sunan takamaiman wurare, ƙungiyoyi, ko mutane: Wadanda zasu goyi bayanku a gaba zasu so sanin ko wannan korafi yana da alaka dasu ko al'ummarsu. Sanya sunan al'umma ko ƙungiyoyin da abin ya shafa zai dauki hankali. Yi tunani game da amfani da CAPS ko ƙarin alamar ƙa'idar rubutu (!!!) wanda za'a iya fassara shi a zaman taken batun mai ban sha'awa, kuma yana iya zama mara daɗi ga wadanda suke da sha'awar goyon baya a gaba.

## Farawa da kalmar Aikatau

Masu karatu suna son sanin takamaiman canjin da kuke son kawowa don su yanke shawarar ko za su iya sanya hannu kan takardar korafin. Taken mukalar ku shine wurin da za ku maida hankali kan samun mafita anan. Kalmomin aikatau gama gari don korafi sune "tsayawa, ajiye wa, hanawa, bayarwa, adawa, ƙarawa, farawa."

## Yi amfani da farkon jumla

Jawo hankalin mutane ta hanyar sanya taken batun ku mai alamar tausayi da gaggawa. Ku bayyana wanda abin ya shafa da kuma dalilin da ya sa kuka damu. Idan akwai takaimaimai ranaku ko lokaci a kan ƙorafin ku, haɗa wannan da bayanan kuma.

## Zaɓi Mai Yanke Hukunci

Mai yanke hukunci shi ne mutumin da ke kan matsayi da ke da ikon taimakawa wajen aiwatar da canjin da kuke nema. Wannan na iya haɗawa da ɗan siyasa, mai tasiri a cikin al'umma, ko ɗan kasuwa. Da zarar kuna da takamaiman manufa don korafin ku, zaku iya gano ko wanene wannan mutumin (ko mutane) a matsayin wanda ya kamata ku tuntuba. Alal misali, zaɓaɓɓun jami'ai na iya taimakawa da al'amuran shari'a, yayin da shugaban 'yan kasuwa zai iya taimakawa wajen yin canje-canje a bangaren 'yan kasuwa masu zaman kansu.

## Tara bayanai game da zaɓaɓɓen mai yanke hukunci don haɗa shi a cikin ƙorafin

Tare da haɗa adireshin imel na masu yanke hukunci da suka dace, za ku iya sanar da su game da korafin ku kuma ku bai wa masu karatu kwarin gwiwa cewa ƙorafin kuna iya yin nasara.

## Zaɓi mutane, ba rukunin mutane ko ƙungiya ba

Ba kamar ƙungiya ba, zaku iya ɗora alhaki ga wasu mutane kai tsaye. Sanya mai yanke hukunci mutum ko mutane a cikin ƙungiya waɗanda ke da alhakin warware matsalarku ko waɗanda kuke buƙatar shawo kansu. Misali "Honorable John Brown" maimakon "Gwamnatin Tarayyar Najeriya."

## Zaɓi wani wanda ke da alhakin kai tsaye

Yana da kyau a nemi mutanen da za su iya baku abin da kuke so maimakon manyan manyan jami'ai, ko wani da ya shahara a cikin al'umma. Wani mai alhakin kai tsaye zai iya yanke hukunci kuma ya warware matsalarku cikin sauri. Sune wadanda basa son hayaniya da matsin lambar jama'a da suke ciki saboda ba su saba da su ba.

## Faɗi labarin ku

Ba da labari yana tsakiyar ci gaban ƙorafi mai nasara. Gaskiya, ƙididdiga, da inda aka samo asalin saƙon suna taimakawa idan za'a hada, amma kuma a yi la'akari da raba ƙwarewar mutum wanda ke taimakawa mutane su haɗa kai da tunanin ku. Yi la'akari da zaɓin kalmar ku da sautin ku dangane da masu sauraron ku. Misali, zaku iya fuskantar iyaye idan takardar ƙorafin ku ya dogara a kan wani dalili kamar lafiyar uwa ko ilimin yara. Ka yi la'akari da ƙimarsu da abubuwan da suka fi ba da fifiko da yadda waɗanda ke da alaƙa da matsalar da kake fatan warwarewa. Hakanan zaka iya haɗa wa da bidiyo don ɗaukar hankalin masu sauraron ku. Kuma ba a buƙatar kashe tarin kudade don ba da labari mai kyau. Tare da kyamarar waya da wasu manhajoji na gyara bidiyo na kyauta, zaku iya bada sha'awar ku kuma a zaburar da wasu su ji kamar ku.



## Ruwa Da Tsakin 'Yan Kasa Ke Yi Don Ganin Gwamnati Ta Sauke Nauyinta Ta Hanyar Shari'a

Najeriya, a matsayinta na mamba a Majalisar Ɗinkin Duniya da Tarayyar Afirka ta amince da manyan tsare-tsare na kare hakkin dan Adam na ƙasa da ƙasa da ke neman ƙarewa da inganta 'yancin ɗan Adam da 'yancin walwala. Babu shakka, tasirin haƙƙoƙin da aka tabbatar a cikin waɗannan hakkin da kuma kundin tsarin mulkin Najeriya ya dogara sosai kan kasancewar isassun matakai da hanyoyin warware ƙorafi don aiwatar da su.

Kotuna na taka muhimmiyar rawa wajen kare haƙƙin ɗan Adam a Najeriya. Kotun ita ce mafi mahimmanci a tsarin mulki da aka tanadar don tabbatar da kiyayewa, da kuma bin ka'idodin haƙƙin ɗan Adam da aka tsara a cikin kundin haƙƙin ɗan Adam daban-daban na duniya da tsarin dokokin mulki.

Dangantakar da ke tsakanin samun adalci ga al'umma da kare haƙƙin ɗan Adam ta samo asali ne daga yadda sai da ɗaiɗaikun mutane suka samu damar hulda da kotuna ne za su iya neman a kare hakkin 'yancinsu. A takaice dai, tsarin doka da hukumomin da ke cikin tsarin na iya zama kamar Katanga ga 'yan ƙasa don samun damar yin hulɗa da kotuna, don haka ba za su iya tilastawa ko kare 'yancin su a matakin farko ba.

## Damar Da 'yan Kasa Ke Da Shi Wajen Yin Ruwa Da Tsaki Ta Hanyar Amfani Da Hanyoyin Shari'a

### Majalisar Lauyoyi dake tallafin shari'a a Najeriya[5]

Majalisar Lauyoyi dake ba da tallafin shari'a a Najeriya tana aiki a duk faɗin ƙasar don ba da agaji na shari'a mai inganci kyauta ga 'yan kasa marasa galihu da ba da murya ga marasa murya. Manufar Majalisar Taimakon Shari'a ita ce Gina ƙasar Najeriya da za a samu daidaiton adalci ga kowa da kowa ba tare da la'akari da banbanci ba, sannan kuma ake mutunta duk wani haƙƙin ɗan Adam, ba shi kariya da kuma kiyaye shi.

[5] https://legalaidcouncil.gov.ng/

## Kungiyar Lauyoyin Najeriya Cibiyar Kare Hakkokin Ɗan Adam ta Najeriya (NBA–HRI)[6]

Kungiyar lauyoyin Najeriya a kodayaushe tana kan gaba wajen inganta kare haƙƙin bil Adama, bin doka da oda da shugabanci na gari a Najeriya. An kafa Cibiyar Kare Hakkokin Bil Adama ta Najeriya (NBA-HRI) don ingantawa da kare martabar doka, 'yancin lauya, da kuma ci gaba da tabbatar da haƙƙin ɗan Adam a Najeriya. Zata inganta mutunta mutuncin ɗan Adam, wanda yake bayyana haƙƙin ɗan Adam zuwa takamaiman ƙa'idoji wajen aiwatar da waɗannan ƙa'idojin a aikace.

Cibiyar tana ba da shirye-shiryen ci gaban fasaha da kuma tsarin samar da albarkatu don bayar da shawarwari a cikin kungiyar lauyoyin Najeriya. Cibiyar ta tanadi sashi mai kula da hakkin bil adama a dukkanin rassanta 120 na Kungiyar Lauyoyin Najeriya a fadin kasar. Cibiyar kare haƙƙin ɗan Adam a matakin reshe tana ƙarƙashin jagorancin mataimakin shugaban NBA na kowane reshe.

Burin Kungiyar Lauyoyi ta Najeriya Cibiyar Kare Haƙƙoƙin ɗan Adam (NBA–HRI) al'ummar da ke kare hakkin dan Adam da kuma tabbatar da 'yancin kan aikin lauya. Al'ummar da ke da damar samun adalci ba tare da wata tangarɗa ba da kuma kare haƙƙin bil'adama da mutuncin mutane masu rauni.

6 https://nbahri.org/

Ruwa Da Tsakin 'yan Kasa Da Bibiyar Gwamnati Hanyar Amintaccen Tsarin 'yan Kasa

Amintaccen Tsarin 'Yan ƙasa, tsarin yarjejeniya ce a rubutacciyar doka tsakanin masu ruwa da tsaki (wato masu shugabanci da wanda ake mulka) da nufin samar da shugabanci na gaskiya da rikon amana. Wani tsari ne na zamantakewa da ƙungiyoyin 'yan ƙasa suka ƙirƙira don bibiyar jami'an gwamnati, 'yan siyasa da shugabanni don auna ayyukansu dangane da isar da ayyukan da ya kamata su yi, nauyin da ya rataya a wuyan su da ayyukan da ya zama tilas su yiwa jama'a. Amintaccen Tsarin 'Yan Kasa, na nufin tabbatar da tattaunawa ta yau da kullun tsakanin 'yan kasa da masu kada ƙuri'a da takamaiman gwamnati ko ɗan takarar siyasa, don cika alkawurransu ga ajandar da za ta kawo ci gaban da suka ayyana a kafar dandalin jama'a. Amintaccen tsarin 'yan ƙasa suna yi ne da niyyar ƙarfafa zama ɗan ƙasa mai ƙwazo, wanda zai haifar da daidaiton dangantaka tsakanin 'yan siyasa da 'yan ƙasa ko shugabannin jama'a, da ba da damar jin muryar marasa galihu a cikin tsari da tsare-tsare. Amintaccen tsarin 'yan kasa yana haɓaka jagoranci mai dogaro da kai yayin da 'yan ƙasa- masu kada ƙuri'a suka fara zabar shugabanni ba don "jawabi mai kyau ba", amma don "ayyukan su" da damar jagoranci da gudanar da mulki. Amintaccen tsarin 'yan kasa na ba da tsari wanda sa hannu zai iya faruwa a matakai daban-daban kuma 'yan ƙasa za su iya shiga don samun kyakkyawan sakamako.

Matakan amintaccen tsarin 'yan kasa sun ƙunshi matakai biyar na ayyuka da suka haɗa da mataki kafin lokacin yin zaɓe da bayan an yi zaɓen.

## Matakin share fage kafin zaɓe

### Mataki 1- Kirƙirar Amintaccen Tsarin 'Yan Kasa

Tsarin ya ƙunshi jerin shawarwarin sassa a matakin al'umma/ mazaɓa, aƙalla wata guda kafin fara yaƙin neman zaɓe. An shirya amintaccen tsarin 'yan ƙasa a matsayin wata ma'ana ta gamayya, haɗin kai, abubuwan fifiko na ƙungiyoyin zamantakewa da tattalin arziki daban-daban kamar manoma, leburori, mata, matasa, masu sana'a, da sauransu kuma ana magana da su da 'yan takaran siyasa.

### Mataki na 2 – Dandalin 'Yan Takara

Dandalin yana tattaro duk 'yan takarar zaɓe domin yin mu'amala da 'yan kasa na karkara. A wurin taron, ana gabatar da amintaccen tsarin 'yan ƙasa tare da neman martani daga 'yan takara. Kasancewar wakilan kafafen yada labarai a dandalin 'yan takara na da matuƙar muhimmanci wajen inganta harkar, da fadada yada labarai ga jama'a da kuma tattara bayanan da aka gudanar, tare da yin yarjejeniyoyin da aka rattaba hannu da kuma alƙawurran da aka ɗauka.

## Mataki na 3- Sa hannu kan Amintaccen Tsarin 'Yan Kasa

Wannan mataki ya ƙunshi rattaba hannu kan yarjejeniya tsakanin masu kada ƙuri'a 'yan ƙasa da 'yan takara. Amintaccen tsarin 'yan kasa ya tanadi yarjejeniya tsakanin 'yan takara da masu kaɗa ƙuri'a, ta yadda 'yan takarar, idan aka zabe su, za su amince a tuhume su ta hanyar ci gaba da tantance ayyukansu na jama'a.

## Mataki bayan zaɓe

Ayyuka a wannan mataki suna farawa ne bayan zaɓaɓɓun jami'an da aka zaɓa sun karɓi ofisoshin su kuma galibi suna haɗa kai da masu yin doka don neman ƙudirin doka da tsara tanadin amintaccen tsarin 'yan ƙasa tare da kason kasafin kuɗin shekara.

## Mataki na 4- Bibiyar nasarori da auna su

Manufar dandalin jama'a ita ce auna ainihin ayyukan jami'an aka zaɓa, dangane da sadaukarwar da suka yi kafin zaɓen game da ajandar jama'a da kuma sharuddan amintaccen tsarin 'yan kasa da suka yarda.

## Mataki na 5- Kirƙirar amintaccen tsarin 'yan kasa

Wannan tsari ne mai tsauri inda ƙungiyoyin fararen hula da gangan zasu ƙaddamar da kamfe don matsin lamba ga wakilan al'umma saboda su zartar da doka don kafa amintaccen tsarin 'yan kasa tare da kason kasafin kuɗin aiwatar dashi.

## Amfanin Amintaccen Tsarin 'Yan Kasa

Amintaccen tsarin 'yan kasa na taimakawa wajen rage cin hanci da rashawa da haɓaka gaskiya, samun dama, samun martani da bibiyar 'yan takarar siyasa da jami'an gwamnati. Amintaccen tsarin 'yan ƙasa sun kuma yi rigakafin munanan ayyuka da dama kamar cin dukiyar jama'a, jinkirin /rashin yin aiki, rashin tsari ko kasafin kudi da aiwatar da ayyuka da rashin da'a na jami'an gwamnati. Ko da a cikin mahallin ƙalubalen da za a fuskanta, hanyoyin ƙirƙira da tsayin daka sun yi nasara wajen inganta tsarin bayyanawa jama'a da samar da martani. Amintaccen tsarin 'yan kasa na cikin tsare-tsare masu ƙarfi don gina manufar siyasa da tasa bukatan talakawa a gaba da manufofi masu sassauci ga al'umma yayin da kuma suke ingizo wajen tabbatar da gaskiya a cikin tsarin zabe da kuma adawa da kudi don neman mukaman siyasa.

## Kammalawa

Dimokuradiyya tana faruwa ne a mahadan 'yan ƙasa da cibiyoyi. Kamar sabbin abubuwan ke faruwa a fasahar zamani, cibiyoyin wakilai, da hanyoyin haɗin kai ke sauya siyasa a kowane mataki, haka ma za su sake fayyace yadda 'yan ƙasa da gwamnatoci ke hulɗa da juna. Kamar yadda ainihin alaƙar mulkin dimokuradiyya ke nuna alamun lalacewa, sababbin ƙirƙire-kirkiren zamani a sararin gwagwarmaya sun bunƙasa. Ko ta hanyar haɓakawa ko amfani da sabbin hanyoyin sadarwa da fasahar sadarwa ko kuma ta hanyar amfani da ƙarfin ƙungiyoyin gwagwarmaya don haifar da sauye-sauyen siyasa, 'yan ƙasa a duk faɗin duniya suna ƙoƙarin sabunta mu'amala tsakanin mutane da siyasa. Amma duk da haka yayin da waɗannan sabbin hanyoyin sadarwa da hanyoyin ke canza zance na jama'a, gwamnatoci da cibiyoyi sun fuskanci koma baya sosai wajen ruguma da rashin gogewar don daidaitawa da waɗannan sabbin hanyoyin haɗin gwiwa.

Dimokuraɗiiyya mai fa'ida tana buƙatar hadakar 'yan ƙasa masu kishi yayin zaɓe da tsakanin zaɓe. A cikin tsarin wakilci, ana gudanar da wannan ta hanyar masu shiga tsakani, gami da cibiyoyi na wakilai na ƙasa da, ƙaruwar, ƙungiyoyi da dandali masu zaman kansu. Don tsarin dimokuraɗiyya ya yi aiki a matakin da ya dace, dole ne 'yan ƙasa dake sanin tsarin siyasa su shiga cikin kowane matakai da matakan tsara manufofin 'yan siyasa da yanke hukunci, gami da ayyuka masu mahimmanci kamar hanyoyin zaɓe, zaman lafiya da gina tsarin mulki. A yau, 'yan ƙasa suna kusantar kawo canji ta hanyar ƙirƙira da ƙirƙiro sababbin hanyoyin hulda da wakilci. Buƙatun ƙarin iko a kan rukunin wakilai, ƙarin riƙon amana a cikin gwamnati da ƙarin hulda mai ma'ana fiye da zaɓe, 'yan ƙasa suna ƙoƙarin yin tasiri kan yadda ake ƙirƙira manufofi da siyasa don kaddamarwa. An canza wannan tsari sosai ta hanyar sabbin hanyoyin fasaha waɗanda suka ba wa ƙarin 'yan ƙasa damar bayyana ra'ayoyinsu a cikin muhimman tattaunawa na jama'a waɗanda ke da yiwuwar yin tasiri ga manufofin siyasa da sakamakon siyasa. Matsin lamba don karɓar karuwar shiga fannin da canza buƙatun 'yan ƙasa, da kuma koma baya ga fahimtar nisanta tsakanin 'yan ƙasa da ƙwararrun 'yan siyasa yana samar da gurabe don sauye-sauyen tsare-tsare a ƙasashe da yawa, musamman a matakin jama'ar karkara.

# Karin Bayanai

Change.Org[7]: Change.org shafin yanar gizo ne wanda ke ba masu amfani damar shiga don kirkirar korafi da kuma sanya hannu ga ƙorafin da wani ya gabatar don karfafa al'amura na cigaba a zamantakewar al'umma ta hanyar wayar da kan jama'a da kuma tasirantar masu yanke hukunci..

Tracka[8]: Tracka wata manhaja ce don al'umma ta 'yan ƙasa masu himma da ke bibiyar aiwatarwa na ayyukan gwamnati a cikin al'ummarsu don tabbatar da an isar da su kamar yadda aka tsara.

Shine Your Eye[9]: Shafin yanar gizo ne wanda yake dandalin sadarwa da ke taimaka wa 'yan ƙasa neman zaɓaɓɓun jami'ai da ke wakiltarsu a kowane mataki na gwamnati tare da basu damar haɗa su.

AdvoKC[10]: Wata manhaja ce da take dandalin sadarwa da aka kafa don taimakawa 'yan ƙasa shiga da damar bin diddigi da kuma bibiyar zaɓaɓɓun jami'an da suka zaba.

PLAC BillsTRACK[11]: Manhaja ce a shafin yanar gizo wanda ta ƙunshi tsarin "ainihin lokaci" wanda ke ba hukumomin jihohi damar bibiyar doka a hanyar tsarin majalisa. Yana samuwa a kowane lokaci daga kowace na'ura mai haɗe da kafar sadarwar intanet.

Africa Check[12]: Africa Check, Wata ƙungiyar kafar sadarwa ce mai zaman kanta ta farko a nahiyar, wacce ƙungiyoyin jin kai da masu ba da agaji ke tallafawa, an kafa ta a Afirka ta Kudu a cikin 2012.

FactCheck Hub[13]: FactCheckHub: Wata kafar sadarwa ce da Cibiyar Nazarin Bincike ta Duniya (ICIR) ta ƙirƙira da nufin yaƙar labaran da aka yaɗa dan yaudarar jama'a wanda sukai kama da gaskiya a cikin al'umma. An kafa ta a watan Mayu 2020 tare da hedikwata a Babban Birnin Tarayya - Abuja, babban birnin Najeriya, kuma ƙungiya ce mai zaman kanta, mai binciken ƙwaƙwaf daga Afirka.

FactCheck Elections[14]: Bin Diddigin Gaskiyar Zaɓuka, Mu dandalin bin diddigin bayanai ne mai zaman kansa, mara nuna ɓangaranci kuma ba a yi shi don neman riba ba. Burinmu na farko shine tabbatar da iƙirari da kuma ƙaryata labaran ƙarya game da ayyukan zaɓe a Najeriya ta hanyar amfani da bincike, bayanai da na'ukan amfani da kayan fasaha.

DUBAWA[15]: Wani shiri ne mai zaman kansa na Afirka ta Yamma mai binciken tabbatar da gaskiya, wanda Cibiyar ƙirƙire-ƙirƙire da Ci gaban Aikin Jarida (CJID) ta ƙaddamar kuma ta sami goyon bayan manyan ɗakunan yaɗa labarai da ƙungiyoyin jama'a a Yammacin Afirka don taimakawa haɓaka al'adun gaskiya a cikin manufofin jama'a, da aikin jarida. Tana da rassa a Najeriya, Ghana, Saliyo, Laberiya da Gambia.

---

7 https://www.change.org
8 https:tracka.ng/#/home
9 https://www.shineyoureye.org/
10 https://www.advockc.org/
11 https://placbillstrack.org
12 https://africacheck.org/
13 https://factcheckhub.com/
14 https://factcheckelections.org/
15 https://dubawa.org/

BRAIN BUILDERS
YOUTH DEVELOPMENT
INITIATIVE

# Takardar Jagora ga 'yan Kasa domin Bibiyan Hakkokinsu

Sponsored by: LEAP AFRICA, NIGERIA YOUTH FUTURES FUND